*KASHI NA DAYA*
*YESU YA YI GIRMA*

Darasi na 1

# AN KAI YESU A HAIKALI

Luka 2:21-39




## YESU MAI CETO

**ME MUKE SO YARA SU KOYA A WANNAN DARASI?**

Za su:

- tuna cewa Yesu ya zo don ya kawo ceto.
- so su bayyana labari mai dadi na ceto kamar yadda Saminu da Hannatu suka yi.

**HADDACEWA**

"Nan take ita ma, ta yi wa Allah godiya, ta kuma yi maganar Dan yaron nan ga dukan masu sauraron fansar Urushalima."

Luka 2:38

# SHIRIN MALAMI



### *NAZARIN LITTAFI MAI TSARKI*

Yin kaciya alama ce da ta nuna Bayahude ne. Ana yinsa kwana 8 bayan haifuwa. A wannan rana ce za a rada wa jariri suna. Radin suna a wancan zamani mai yiwuwa yana kama da namu a yau.

Suna tana da ma'ana. Man'anar 'Yesu' ita ce 'Mai Ceto'. Sunan Yesu ya bayyana halin rayuwarsa – ya kawo ceto.

Abubuwan da Saminu da Hannatu suka fada bayan sun ga Yesu, sun zo daidai da abin da mala'iku suka fada kafin haifuwar Yesu. Wadannan abubuwan da aka fada a kan Yesu ya nuna Yesu ne wanda annabawan Tsohon Alkawari suka yi rubutu a kansa.



### *ME AKE BUKATA DOMIN DARASIN NAN?*

1. Hoto na 1, 'Saminu ya ga Yesu' domin LABARIN L.M.T. Kashi na 3.
2. A yanka takarda daidai hoton kafan mutum. Rubuta, '**Yesu ne Maiceto**'. Za ka nuna wannan bayan an gama darasi.
3. Ku koyi raira taken waka na wannan shekara (shafi 5) da waka na wannan darasi.
4. Domin GABATARWA, kawo doli-doli na yaro.



## LOKACIN DARASI

**Gabatarwa**

### A FARA DA AD-

- FADI wani abu a kan radin suna da yara sun kan halarta.
- TATTAUNA ma'anar sunaye.
- KWAIKWAYO – Yara 2 su zama iyaye, suna rike da doli-dolin jariri. Yara su yi kamar suna rada suna.
- YI TAMBAYA
  *Ko sunaye a kowane lokaci suna da ma'ana?*
  *Ko ka san ma'anar sunanka?*



## Labari daga Littafi Mai Tsarki — Luka 2:21-39

### 1. Bukin radin suna (aya 21)

- Yusufu da Maryamu sun bi al'adun Yahudawa.
- An rada wa Yesu suna tare da yi masa kaciya a kan rana ta 8.
- Yusufu da Maryamu sun rada masa suna 'Yesu", kamar dai yadda mala'ika ya fada.
- Tuna wa yara cewa ma'anar sunan 'Yesu' shi ne 'Mai ceto'. Mala'ika ya ce Yesu zai kawo ceto daga zunubi.

### 2. Mika Yesu Jariri a haikali (aya 22-24)

- Bayan kwana 40, Yusufu da Maryamu sun kai Yesu haikali.
- Sun mika shi ga Allah.
- Za su mika hadaya bisa ga al'adar Yahudawa.
- Sun mika tattabarai 2. Bisa ga dokar Yahudawa, wannan ne abin da talaka zai bayar. Wannan ya tuna mana cewa Allah ya zabi iyali talakawa domin a haifi Dansa..

### 3. Siminmu ya gane Yesu (aya 25-35)

- Saminu wani tsohon mutum ne a Urushalima. Ya yi ta jiran Allah domin ya aiko da Almasihu.
- Da Saminu ya ga Yesu Jariri, Ruhun Allah ya fada masa cewa wannan shi ne Almasihu.
- Saminu Ya rike Yesu Jariri ya fada wa Allah cewa, "Na gode".
- Saminu ya fada wa Maryamu da Yesu cewa za su sha wahala kwarai.
- NUNA Hoto na 1.

### 4. Hannatu ta gode wa Allah (aya 36-39)

- Wata da ta ga Yesu a haikali ita ce Hannatu.
- Hannatu tana addu'a tare da jira na lokaci mai tsawo domin zuwan Almasihu da aka alkawarta.
- Da Hannatu ta ga Yesu, sai ta gode wa Allah sabo da Yesu zai kawo wa Yahudawa albarka.
- Ta yi ta fada wa mutane labarin Yesu Jariri.
- Yusufu da Maryamu sun koma gidansu.
- Yesu ya girma, ya yi karfi.

**Kwaikwayo:** Yara su kwaikwayi labarin. Yaron da ya iya karatu sosai, ya karanta kalmomin Saminu (aya 29-32, 34-35).

## Karshen Darasi … .

* Abubuwa da Saminu da Hannatu suka fada sun tuna mana abin da mala'ika ya fada kafin a haifi Yesu: Yesu Dan Allah ne wanda aka aiko domin ya zama Maiceton duniya.
* Hannatu nan da nan ta ci gaba da fada wa mutane cewa Yesu shi ne Maiceto wanda Allah ya alkawarta shekaru masu yawa da suka shige.

► **Ka koyar da Haddacewa yanzu (Luka 2:38).** Tuna wa yara abubuwa 2 da Hannatu ta yi: (1) "gode wa Allah" (hada hannu tare don yin addu'a); da (2) fada wa mutane labarin Yesu (sa hannu a baki kamar kana yin magana).

**AYYUKA:** Wasu yara su zama masu daukan labaru. Su fada ko su rubuta labarin haifuwar Yesu da tafi yarsa haikali idan za su ba da labari a radiyo ko talibijan.

**ADDU'A:** Ku gode wa Allah domin mun iya yin addu'a cikin 'sunan Yesu'.

**WAKA :** "Yesu, Mai Ceto, Mai Cetonmu,
Za mu yabe ka har abada ……." ♫

**YIN TAFIYA TARE DA YESU A WANNAN MAKO:** Nuna misalin kafa da ka gyara**,** 'Yesu ne Maiceto'. Mu gode wa Allah saboda ya aiko Yesu, kuma su fada wa wasu cewa Yesu ya zo ya cece mu.